# Takardar Aiki: Yaya hanyar damawa da mai ruwa da tsaki take kama?

Jadawalin da ke ƙasa zai taimaka muku wajen shimfiɗa tubalin dubara na damawa da mai ruwa da tsaki da za a yi amfani da shi a cikin furojet ɗinku ko aikinku gabaɗayansa. Haka kuma, tubali ne sannan matakin farko na samar da shirinku na damawa da mai ruwa da tsaki, wanda za a aro zuwa ga dabararku da zarar kun gano masu ruwa da tsaki na furojet ɗinku.

| MANUFA | MATAKAN DA YA KAMATA A ƊAUKA | TAMBAYOYIN DA KE JAGORANCI/MATAKAI |
|---|---|---|
| **Kimanta:** Kayyade amfanin masu ruwa da tsaki | 1. Aunawa<br>2. Ganowa da damawa da masu ruwa da tsaki<br>3. Samun bayanai | • Waɗanne ne manufofinku na kaitsaye da na kaikaice domin damawa da sauran masu ruwa da tsaki a cikin shirinku/aikinku? Waɗanne manyan masu ruwa da tsaki ne ke aiki a kan lamurran ko muhimman lamurran da ke da alaƙa? Ko kuna magana/aiki da su?<br>• Ko wani daga cikin waɗannan masu ruwa da tsaki (har da waɗanda ba ku taɓa wata alaƙa da su ba) kan ƙara wata daraja ga furojet ɗinku/shirinku?<br>• Waɗanne bayanai ne abokan hulɗa/masu ruwa da tsaki za su iya wayar da kai a kansu ta la'akari da ƙokarin da suke da shi a yanzu?<br>• Ta yaya kuke iya gina ƙoƙarin masu ruwa da tsaki, saboda haka sai ya kasance suna iya taka rawa mai tasiri a cikin shirinku?<br>• Waɗanne ne wasu daga cikin bukatocinku/gibi ta la'akari da ƙokari da ƙwarewar da za su iya zama cikas ga shirinku sannan ta yaya za ku iya amfani da ƙoƙarin sauran masu ruwa da tsaki domin magance waɗannan kalubala?<br>• Ko akwai wasu shafukan intanet tsakanin sauran masu ruwa da tsaki da za ka iya gina a kansu, gyara ko samarwa? |
| **Tsari:** Kirkirar tarayya | 4. Farawa<br>5. Shiryawa<br>6. Tsarawa | • Me zai kasance alaƙar aiki tsakanin masu ruwa da tsaki daban-daban?<br>• Ko dukkan masu ruwa da tsaki sun yarda da manufar ƙulla hulɗa da ƙa'idoji, manufofin furojet, ToC, manufofi, sakamakon da ake tsammani, da ma tsarin shiri?<br>• Waɗanne matakai ne za a ɗauka, sannan wane mai ruwa ko masu ruwa da tsaki ne za su ɗauke su? Ko dukkan masu ruwa da tsaki sun yarda da tsarin aiki, lokacin da aka kayyade, da sauransu?<br>• Mene ne zai kasance tsarin kula da shirinku? Mene ne matsayi da alhakin da aka ɗora wa kowanne mai ruwa da tsaki? Ko dukkan masu ruwa da tsaki sun yarda da matsayinsu da alhakin da aka dora musu? |
| **Ɗabbaƙa:** Ɗaukar mataki | 7. Ɗabbaƙawa<br>8. Kulawa | • Waɗanne ayyuka ne ake bukatar ɗabbaƙawa domin ƙaddamar da shiri?<br>• Wa ke kula da dangantaka tsakanin masu ruwa da tsaki? Ta yaya masu ruwa da tsaki ke sadarwa a tsakaninsu? |
| **M&E, da Koyo:** Sa ido da koyo | 9. Dubawa/Kimantawa | • Ko Masu ruwa da tsaki sun yi aiki yadda ya dace, sannan sun yi ƙoƙarin sauke alhakin da aka ɗora musu?<br>• Ta yaya sauye-sauyen ƙulla hulɗa suka ba kowane mai ruwa da tsaki karfi ko ta yaya suka kawo cikas ga ɗabbaƙar da ayyuka?<br>• Ko muna bukatar ci gaba da aiki da abokan hulɗa iri daya? Ko za mu shigar da ƙari/wasu masu ruwa da tsaki ko kai ƙarshen hulɗar da muka ƙulla da su? |